# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Lokacin da Allah ya Halicci komai







**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Byron Unger; Lazarus Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Bob Davies; Tammy S.**

**Fassarawa: Maren Dameng Daniel**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2020 Bible for Children, Inc.**

**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**

Wa ya halicce mu? Littafi mai tsarki maganar Allah, ya fada mana yadda aka fara yin hallita. Can da jimawa, Allah ya hallici mutum na farko ya saka masa suna Adamu. Allah ya hallici mutum daga cikin kura na kasa. Da Allah ya hurawa Adamu rai sai ya kasance a raye. Ya ga kansa a cikin kyakkyawar gonar da ake kira Eden.



Kafin Allah ya hallici Adamu, ya hallici kyakkyawar duniya cike da abubuwa masu ban mamaki.  Hawa-hawa Allah ya hallici wurare masu burtsi da kyawawun sarari, furanni masu kamshi, da bishiyoyi masu tsayi, tsunstaye masu gyalgyalina fukafukai, gudan zuma masu harbi, da manyan hallittun kifaye, da dodon koɗi masu



santsi.  A taƙaice Allah ne ya hallici komai kuma akwai komai.

A farkon farawa, kafin Allah ya hallici wani abu, babu komai sai Allah kadai.  Babu mutane ko wurare ko abubuwa.  Babu komai.  Babu haske babu duhu.  Babu sammai babu kassai.  Babu jiya babu gobe Allah ne shi kadai babu farkon sa.  Sai Allah ya wanzar.



**A farkon farawa Allah ya halicci aljanna da duniya.**

Duniya ba ta da siffa, sarari ce kawai, duhu kuwa ya lullube fuskar zurfin teku. Allah ya ce, “Haske ya kasance.” Allah ya ce, “Bari haske ya kasance,” sai kuwa ya kasance.



**Sai kuwa ya kasance ga hasken. Allah ya raba tsakanin hasken da duhu, yace kira hasken, "yini," duhu kuwa, "dare." Kuma maraice, da safiya, sune rana na farko.**



A rana ta biyu, Allah ya halicci ruwa, kogi, teku da qorama ajere a garkashin aljanna.  A rana ta uku kuma sai Allah yace, “Busasshen kasa ya kasance.”  Sai ya kasance.



Allah ya umurci ciyawa da furanni, kananan tsirrai da bushiyoyi su fito, sai suka fito. Sannan Yinin da Safiya sune rana ta uku. Ga maraice, ga safiya, kwana na uku ke nan.



Sa'annan Allah ya halicci Rana da Wata da 5aurari masu yawa wanda ba mai iya yirga su.  Yini da Safiya sune rana ta hudu.



Halittun cikin ruwan
teku da kifaye manya da
tsuntsaye  sune na gaba
a jerin abunda Allah zai
halitta.  A rana ta biyar
ya halicci, manyan kifi
ƙurunku da ƙananan kifi
tarwaɗa, Jimina da tsuntsu
kanari.  Allah ya halicci
dukkanin launi kifi su cika
ruwa sannan ya hallicci
dukkan launin tsuntsaye
suyi shawagi a kan ruwa
da sama.  Yini da Safiya
sune rana ta biyar kenan.



**Bayan haka Allah yayi magana yace, “kasa fidda abubuwa masu rai” duk wani abu mai rai duniya ta fidda masu rai bias ga irinsu.  Duk launin dabbobin gida, ƙwari da kuma dabbobin jeji manya da ƙanane, da kowane irin abu mai rai bisa kasa.**

**Da yini da safiya, kwana na shida kenan.**



Allah kuma ya ce, bari mu yi mutum cikin siffarmu, da kamanninmu, su mallaki kifayeni da suka a cikin teku, da tsuntsayen sararin sama, da dabobbi, da dukan duniya, da kowane abu mai rarrafe da yake rarrafe bisa kasa, “HAKA NAN FA,” ALLAH YA HALICCI MUTUM, YA HALLICE SHI YADDA YAKESO YA GANSHI.



**Ubangiji Allah ya yi wa mutumin umarini, ya ce, “kana da yanci kaci daga kowane itacen da yake a gonar, Amma kada kaci daga itacen sani, nagarta da kuma mugunta, gama a ranar da ka ci lalle za ka mutu.”**



Saan nan sai ubangiji Allah ya ce, “Bai dace mutum ya zauna shi kadai ba,zan yimasa mataimakin da ya dace dashi.” Sai Ubangiji, ya kawo kowace dabba da tsuntsaye wurin mutumin, ya ga yadda zai kira su, duk abin da mutumin ya kirawo shi to kuwa, sunansa ke nan. Mutumin ya bai wa dabbobi duka suna, amma ba a sami mataimaki wanda ya dace da mutumin ba.



Sai ubangiji Allah yasa Adamu bacci mai nauyi. Lokacin da yake bacci ubangiji Allah ya cire daya daga cikin hakarkarinsa ya cike wurin da nama, hakarkarin nan kuwa da ubangiji Allah yacire daga mutumin ya yi mace das hi ya kuwa kawo tag a mutumin. Don daga cikin mutum aka ciro ta.



Allah ya halicce komai a cikin kwana shida. Sai Allah ya albarkace rana ta bakwai, ya sanya shi ranar hutu. A cikin gonar Eden, Adamu da matar sa Hauwa'u suna cikin matukar farinciki da biyaya ga Allah. Allah kuwa shi ne ubangijin su. Mai biya masu buƙatun su da kuma abokin su.



# Lokacin da Allah ya Halicci komai

## Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

## a na samu a

## Farawa 1-2

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah: Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**